Njinga & Sepé: Revista Internacional de Culturas, Línguas Africanas e Brasileiras
São Francisco do Conde (BA) | vol. 5, nº Especial I | p. 24-32 | jan./ jun.2025.

# Ra'in Zahiranci a Cikin Waƙar Baka: Tsokaci a Kan Waƙar *Mai Akwai da Babu* ta Alh. (Dr) Adamu Ɗanmaraya Jos

# O Sentido da Existência na Poesia Oral: Uma Reflexão sobre a Poesia do Presente e do Não-Presente por Alh. (Dr.) Adamu Danmaraya Jos

**Isa Umar Al-Musawi, M.A. (Hausa Culture)** *
ORCID iD https://orcid.org/0009-0006-9872-0277

**TSAKURE**
Wannan bincike mai taken Ra'in Zahiranci a Cikin Waƙar Baka: Tsokaci a Kan Waƙar Mai Akwai da Babu ta Alh. (Dr) Adamu Ɗanmaraya Jos, ya yi dubin irin gudummawar da mawaƙan baka na Hausa suke bayarwa ta fannin wa'azantarwa da hannunka mai sanda ga al'umma musamman masu kuɗi. Wannan dubi kuwa an yi shi ne ta ɓangaren tarbiyya, domin gyara kayanka bai zamo sauke mu raba ba. Kamar yadda yake cikin waƙar mai akwai da babu. Makasudin wannan aikin shi ne bayyanar da irin gudummawar da waƙa musamman ta baka take bayarwa ga al'umma ta fannin gyaran hali. An yi amfani da wallafaffun littattafai masu dangantaka da aikin sai kuma aka nazarci ita waƙar, a matsayin hanyoyin bincike. Sannan binciken ya kawo bayanin ra'in zahiranci da manufofinsa kamar yadda Mustapha (2013) da Gambo (2017), suka kawo a cikin ayyukansu, domin a wannan ra'in ne aka ɗora aikin. A cikin binciken an kawo misalan yadda mai akwai yake kallon maras shi, sannan aka yi ɗan jan hankali ga shi mai akwai domin ya gane dukiyarsa ba ta sanya Allah ya fifita shi a kan talaka ba, wadda daga ƙarshe ko mutuwa ya yi launi da adadin yadin da za a nannaɗe shi da wadda za a naɗe talakan da shi duk iri ɗaya ne, sannan dukkansu biyun a rami za a binne su bayan mutuwarsu.

**FITILUN KALMOMI**
Talauci, Wadata, Waƙar Baka, Zahiranci.

**RESUMO**
Esta pesquisa, intitulada Ra'in Zahiranci a Cikin Waqar Baka: Tsokaci a Kan Waqar Mai Akkaiwa da Babu, do Dr. Adamu Danmaraya Jos, examinou a contribuição dos poetas orais hauçás no campo da pregação e do ensino à comunidade, especialmente aos ricos. Este estudo foi realizado sob a perspectiva da educação, pois consertar seus pertences não é algo que possamos compartilhar. Como no poema Mai Akkaiwa da Babu, o objetivo deste trabalho é revelar a contribuição que a poesia, especialmente a poesia oral, traz à comunidade no campo da reforma moral. Livros publicados relacionados à obra foram utilizados e o próprio poema foi analisado como métodos de pesquisa. O estudo, então, explicou o conceito de Zahiranci e seus objetivos, conforme Mustapha (2013) e Gambo (2017) trouxeram em suas obras, pois é nesse conceito que o trabalho se baseou. No estudo, foram dados exemplos de como os ricos olhavam para os pobres, e então foi dada uma pequena atenção ao rico para que ele percebesse que sua riqueza não fazia

* Department of Arts Education (Hausa Unit), School of Undergraduate Studies, Peacock College of Education, Jalingo, An Affiliate of Taraba State University, Jalingo, Taraba State, Nigeria, E-mail: isaumaralmusawi@gmail.com

com que Deus o preferisse aos pobres, que no final, ou na morte, a cor e a quantidade de tecido a ser enrolado e aquele a ser enrolado no pobre são todos iguais, e ambos serão enterrados em um buraco após a morte.

**PALAVRAS-CHAVE**
Pobreza, Riqueza, Poesia Oral, Manifestação.

**Gabatarwa**

Waƙa daɗaɗɗiyar aba ce ga rayuwar ɗan'adam, domin babu wadda zai iya cewa ga lokacin da ɗan'adam ya fara rera waƙa. Wasu masana suna ganin waƙa ta fara samuwa ne tun lokacin da aka fara samun iska tana kaɗa ganyaye da rassa suna gugar juna, nan aka fahimci waƙa suke yi. Waƙa tana nufin wata hikima ce ta zaɓen kalmomi da rera su, saɓanin yadda ake aiwatar da su a magana. Saboda haka, waƙar baka ta Hausa ta jima tana taka muhimmiyar rawa a cikin rayuwar Hausawa (Gambo, 2017).

**Ra'in Zahiranci**

Ra'i falsafa ce da ake amfani da ita wajen faɗar gaskiya da yanke hukunci bisa gaskiya na faruwar wani abu ko wata matsala ta rayuwa (Ado, 2017). Ita kuwa CNHN (2006), ta ba da ma'anar zahiranci da cewa haƙiƙa ko gaskiyar abu. Saboda haka ra'in zahiranci, hanya ce ta bayyana rayuwar mutum ko al'umma ta gaskiya ko ta zahiri ba tare da ragi ko ƙari ba.

Ra'in Zahiranci an ƙirƙiro shi ne a wurin ƙarni na goma sha tara (19th C), a Faransa cikin shekarar 1830. Maƙirƙiran wannan ra'in kuwa sun haɗa da Honor de Balzac da Gustave Flaubert da Anton Chechov da Geeorge Eliot wacce ta rubuta Adam Bebe a shekarar 1859 da Mark Twain da William Dean Howells da babban ɗan zahirancin nan Herry James (Gambo, 2017).

Mazhabar ta yaɗu daga ƙasar Faransa zuwa Ingila da Amurka a farkon ƙarni na ashirin (20th C). A Ingila an samu tartsatsin zahiranci a ayyukan Chalse Dickens da William Makepeace Thackery da George Moore da sauransu. Mazhabin zahiranci yana ɗaya daga cikin mazhahobin tarken adabi da ke duba wasu abubuwa na rayuwa a cikin al'umma, musamman rayuwa ta zahiri ta hanyar aikace-aikacen adiban duniya. Kasancewarta mazhabar tarke sai ta samu karɓuwa ga matarka masu sha'awar duba halayen al'umma daban-daban. Lokacin da Mazhabar ta ƙara ƙarfafa sai aka samu ɓullowar matarka masu la'akari da halayen zahiri a cikin littafin hira da na wasan kwaikwayo (fim) masu kama da na tsafi (margical realism). Sun kasance suna fito da tartsatsin tsafi da ke fitowa cikin wasu ayyukan adabi masu halaye na zahiri, waɗanda suke akasarinsu na Latin Amurka ne a ƙarni na ashirin (20th C). An kuma samu ɓullowar ƙungiyar zahiranci ta tsarin zaman jama'a (socialist realism) a watan Agustan shekarar 1934, a babban taron adiban Rasha. Ƙungiyar tana da ra'ayin cewa tarke da adabi lallai ne su zama masu haskaka tunanin sauyi na mutanen zamani, tare da bayyana abin da ke aukuwa na gwagwarmayar 'yan sauyi a cikin al'umma (Reymond, 2009).

A ɓangaren adabin Hausa kuwa, marubuta da dama suna yin rubuce-rubuce game da halin rayuwar al'ummar Hausawa da take gudanarwa a zamaninsu, domin ƙoƙarin fito da wasu matsalolin da ke aukuwa a cikin al'ummar da nufin magance su. Wasu matsalolin ƙirƙiransu aka yi, kuma suna da nasaba da halin rayuwar da mutum ya samu kansa ya kuma kasa daurewa.

**Wasu Daga Cikin Manufofin Ra'in Zahiranci**

- Tana ƙimanta duniyar ɗan'adam da abinda yake faruwaa cikinta, da son bayyana su yadda ya dace.

- Tana bai wa adibai ƙarfin niyyar gamsar da makaranta irin halin rayuwar da al'umma take ciki (Smith, 1985).
- Tana ƙoƙarin fito da abin da ya faru ko yake faruwa, ba wadda ake buri ko wadda ake ra'ayi ko fatan aukuwarsa ba (Ilorin, 1994).
- Tana sauƙaƙa salon littafi da hoton tunani da ƙara mayar da kai a kan halin talauci da abubuwan da ke wakana a cikin al'umma.
- Tana kallon adabi a matsayin mai kwaikwayon rayuwa ta zahiri a al'umma da ƙarfafa amfani da tunanin ɗan'adam tare da neman gano gaskiyar lamura tare da tsayawa a kan batun gaskiya, maimakon amfani da salo ko balaga ko zubi da tsari a cikin adabi (Gambo, 2017).
- Tana nuna faruwar abubuwa na zahiri a cikin al'umma kamar wahala da musgunawa da danniyar shugabanni da yadda ake faɗarsu daidai-wa-daida ba tare da wasu kwane-kwane ba, saboda neman gyara da samar da al'umma ta gari.
- Tana nazarin halayen ɗan'adam da wasu abubuwan da tunanin adibi yake tsinkaya na rayuwar yau da kullum, kamar siffanta halin rayuwa ta gaskiya (na zahiri), da yadda ake ba ta muhimmancin gaske a cikin rubuce-rubucen adabi.

**Waƙar Baka**

Waƙa ta rayu tana daɗa bunƙasa da kuma haɓaka har zuwa yau, hakan yana nufin cewa akwai wuyar sanin haƙiƙanin lokacin da aka fara samun waƙar baka kenan. Ko da yake wasu masana suna ganin an fara samun waƙar baka ne ta hanyar kirari yayin farauta ko wurin bautar gargajiya (Gusau, 2005). Masana irin su Gusau (2014), sun bayyana cewa waƙar baka daɗaɗɗiyar aba ce da ta faro tun lokaci mai nisan gaske. Sannan tana da ma'anar magana ce ingantacciya aunanniya wacce ake rerawa kuma mai tsari. Haka kuma za mu iya bai wa waƙa ma'anar cewa wani abu ne da yake zuwa a yayyanke a cikin wani rukuni a jejjere. Yakasai (BSB), yana cewa waƙar baka magana ce a kan sarrafaffiyar murya wacce ake rangwaɗar da murya bisa wani tsari na adabin baka, ya ƙunshi nau'o'in kaɗe-kaɗe da Hausawa suke aiwatarwa cikin harkokinsu na rayuwar yau da kullum. Hausawa sukan yi amfani da wasu abubuwa da dama masu fitar da amo waɗanda suka ƙunshi kayan bugu da da na bushi da kuma wasu da dama da ake gogawa da wasun waɗannan. A wata mahangar kuwa waƙa tana nufin wani furuci ne (lafazi ko saƙo) cikin azanci da ake aiwatarwa ta hanyar rerawa da daidaita kalmomi cikin wani tsari ko ƙa'ida da kuma yin amfani da labaru ko salon armashi (Ɗangambo, 1984).

Wasu kuwa suna ganin waƙa a matsayin wani furuci ne ko saƙo cikin azanci da ake aiwatarwa ta hanyar rerawa da daidaiton kalmomi cikin wani tsari ko ƙa'ida da kuma yin amfani da dabaru ko salon magana. Sannan Gusau (2023), ya bayyana waƙar baka da cewa wani zance ne shiryayye cikin hikima da azanci da yake zuwa gaɓa-gaɓa bisa ƙa'idojin tsari da daidaitawa a jere cikin sautin murya da amsa-amon kari da kiɗa da amshi. Muhammad (2003), da ya tashi cure bayanin waƙa wuri ɗaya sai ya bayyana cewa waƙa magana ce ta fasaha a cure wuri ɗaya a cikin tsari na musamman. Wani masanin kuwa ya bayyana ma'anar waƙar ce a cikin waƙe, inda yake cewa:

*Waƙa da zance dole ne a raba su,*
*Zance daban waƙa ana tsarawa.*
(Ɗangambo, 2007).

Haka nan, game da waƙoƙin baka Gusau (2008), ya yi ƙarin haske da cewa waƙoƙi ne waɗanda ake aiwatarwa cikin harshen Hausa, sannan a sadar da su da ka ta hanyar rerawa. Wannan masani ya bayyana cewa waƙoƙin baka ba rubuta su ake yi ba, a'a ana

sadar da su ne ta hanyar yin amfani da harshen Hausa ba tare da an rubuta su bisa wata takarda ko wanin wannan ba.

### Taƙaitaccen Tarihin Alhaji Adamu Ɗanmaraya Jos

An haife shi a shekarar 1946 a Ɓukur, kusa da garin Jos, Nijeriya, ana ce da shi Adamu Wayya amma an fi saninsa da **Alh. Adamu Ɗanmaraya Jos** mahaifinsa makaɗin fada ne. Ya fuskanci ƙalulabe a rayuwarsa kasancewar mahaifinsa ya rasu tun yana ƙarami, ya tashi ne a hannun mahaifiyarsa, wannan ne ya sanya ake ce da shi ɗanmaraya. Saboda hazaƙarsa hakimin Ɓukur ya ɗauki nauyin kulawa da shi har ya girma. Alh. Adamu Ɗanmaraya makaɗin kutugi ne, sannan shi kaɗai yake sana'arsa ma'ana ba shi da masu yi masa kiɗa ko amshi. Wannan shi ya ba shi damar bayyana hikima da hazaƙarsa a sarari.

Sannan Alh. Ɗanmaraya Jos yakan yi wa kusan kowa waƙa ba sai saraki ko attajirai ba, abubuwa da dama yakan waƙe, sannan ya yi waƙoƙi kusana a dukkan ɓangarorin rayuwa. Hatta lokacin tsanani lokacin yaƙin basasa sai da ya waƙe wannan zamanin. Ɗanmaraya ya yi fice a wannan fage nasa na waƙa wadda har ya kai shi ga samun kyautar girmamawa daga gwamnatin tarayya ta Member of the Order of the Niger (MON) da Officer of the Order of the Niger (OON), da sauransu. Saboda sadaukarwarsa da ƙwazonsa tare da bunƙasa adabi da al'adun Hausawa.

Alh. Adamu Ɗanmaraya ya bar duniya a shekarar a 2015 yana ɗan shekaru 69, ya rasu ya bar wagegen giɓi a fannin adabin Hausa wadda cike wannan giɓi abu mai waya. Waƙoƙin Ɗanmaraya sun haskaka tarihi da rayuwa da ɗabi'un Bahaushe. Ana tsammanin waƙoƙin da Alhaji Ɗanmaraya ya rera a rayuwarsa sun haura 500.

### Makasudin Gudanar Da Bincike

Kamar yadda yake cikin waƙar mai akwai da babu, makasudin wannan takarda shi ne bayyanar da irin gudummawar da waƙa musamman ta baka take bayarwa ga al'umma ta fannin gyaran hali, ba kawai ga masu hali ba, a'a har ma da mabuƙata.

### Hanyar Gudanar da Bincike

An yi amfani da hanyar sauraron waƙar Alhaji Adamu Ɗanmaraya Jos ta *Mai Akwai da Babu* aka yi nazarinta, sannan kuma aka bibiyi wasu littattafai da maƙalu masu dangantaka da *Ra'in Zahiranci* a matsayin hanyar gudanar da wannan bincike.

### Dangantakar Ra'in Zahiranci da Waƙar Alhaji Adamu Ɗanmaraya ta *Mai Akwai da Babu*

Lallai yawancin mawaƙan Hausa suna gabatar da waƙoƙinsu ne bisa abin da yake faruwa na yau da kullum tsakanin al'umma. Kasancewar ra'in zahiranci yana batu ne kan rayuwar gaskiya da haƙiƙanin abin da yake faruwa na daga rayuwar al'umma ta gaskiya ya sanya wannan ra'in yake da dangantaka da wannan waƙa wadda Alh. Adamu Ɗanmaraya Jos ta mai akwai da babu ya gabatar.

### Yadda Adabi Yake Bayyana Gaskiyar Lamari

Mawaƙa sukan bayyana yadda gaskiyar lamari yake, kamar yadda Alh. Ɗanmaraya ya bayyana a wannan ɗiyar waƙar ta farko cikin waƙar mai akwai da babu yake cewa:

1. *Amma mai akwai da babu duka dangantakanku daidai,*
   *Allah ike faɗan haka ba ni nake faɗa ba,*
   *da ni nake faɗan haka da sai ku ƙaryata ni.*

A cikin wannan ɗiyar (1), mawaƙin ya nuna mawadaci da mabuƙaci duk matsayinsu ɗaya ne a wurin Allah, har yake kafa hujja da cewa Allah ne yake faɗin hakan ba wai shi ne ya faɗi ba. Ya ƙara da cewa, da shi ne yake faɗin haka da za a ƙaryata shi. Domin a halin da muke ciki a wannan zamani ana ganin mawadaci yana da wata ƙima a idon al'umma, wadda har takai ana masa gani na daban, yayin da shi mabuƙaci kuwa ake yi masa ganin rago.

**Ta Yadda Adabi Yake Fito da Hoton Tunanin Mai Akwai**

Mawaƙa sukan yi ƙoƙarin fito da tunanin mai akwai domin ya fahimci tarin abin da ya mallaka ba zai sanya ya yi amfani da abu fiye da guda ɗaya saboda wadatarsa ba, kamar yadda hakan ya bayyana a cikin wannan ɗiyar:

2. *Kai mai akwai ka gane idan kai gida talatin cikin guda za ka je ka kwana,*
   *a ɗaki guda kakan kwan a kayin gado guda ɗai,*
   *haka nan wanda bai da komai gida guda za i je i kwana,*
   *a ɗaki guda ikan kwan a gefe guda ikan kwan,*
   *a kayin karauno falle, to in gari ya waye ta nan duka dangantakarku daidai.*

A cikin wannan ɗiyar (2), mawaƙin ya yi ƙoƙarin fito da hoton yadda mai akwai yake ganin kansa, duk da ya tara gadaje a cikin ɗakunan da ya mallaka a cikin gidajensa da yake da su ba zai iya kwana a kan gado ko a ɗaki a cikin gida fiye da ɗaya ba. Haka nan wanda bai da shi, a kan karauno falle ɗaya da kuma gida guda ɗaya zai je ya kwana, kuma da zarar gari ya waye suna da kusancin dangantaka, sadoda dare guda ɗaya suka ratsa zuwa wayewar gari.

Sannan a wannan ɗiyar kuwa ga abin da mawaƙin yake cewa:

3. *In baku ɗan misali kai mai akwai ka gane,*
   *in kana taƙamar akwai ne, ba ka sanya hula goma a kanka kai ɗai,*
   *ai da an ganoka sai a ce wane ya taɓu,*
   *sai dai ka sa guda ɗai haka nan wanda bai da komai,*
   *shi ma i sa guda ɗai matuƙar in yana da hali,*
   *to malam idan ka duba ta nan duka dangantakarku daidai.*

A ɗiya ta uku kuwa, mawaƙin ya ankarar da mai akwai ne da cewa ya tuna cewa shi fa kayinsa guda ne, haka nan wanda bai da shi ma, kayin nasa guda ɗaya ne saboda haka suna da dangantaka. Ya cigaba da cewa, yadda mai akwai zai sanya hula guda ɗaya a kansa, haka nan wanda bai da shi ma hular guda ɗaya zai sanya matuƙar ya samu halin yin hakan. Sannan mawaƙin ya bayyana dangantakarsu guda ce a wannan fannin ta sanya hula guda-guda a kawunansu.

Mawaƙin ya kuma kawo wata ɗiyar da ke magana game da agogo da cewa:

4. *In ba ku ɗan misali da agogon jeka talatin, da agogon sulai talatin,*
   *in wannan i ba da loko daidai, wannan i ba da loko daidai,*
   *in za a dai kira su, sai ka ga sunansu duk agogo.*

Wannan ɗiyar ta 4 tana cewa Agogon jaka talatin (₦6,000) da kuma agogon sulai talatin (₦3:00) matuƙar za su bayar da lokaci guda daidai to ba su da bambanci, domin duk cikarsu za a kira su da agogo. Saboda hakan ne, mawaƙin ya bayyana matsayin da duk agogon suke da shi bai wuce na su kwatanta lokaci ne ba. Saɓanin da suke da ita a wurin tsada (kuɗi) ba shi ne abu muhimmi ba, illa bayar da lokaci daidai.

Lokacin da mawaƙin ya tashi bayani game da nono kuwa, sai ya ce:

5. *In ba ku ɗan misali da nonon sulei talatin da nonon kwabo talatin,*

*in za ka dai sumayi sai ka ga duk dai farinsu daidai.*

Sannan mawaƙin a cikin wannan ɗiyar ta 5 ya yi misali da nonon da aka saya da kuɗi mai yawa (tsada) da kuma wadda aka saya da kuɗi kaɗan (arha), in an gan su duk launi ɗaya suke ɗauke da shi (fari).

Haka nan mawaƙin ya cigaba da jawo hankalin mai akwai da cewa:

6. *Kai mai akwai ka gane, in kana taƙamar akwai ne,*
*ba ka sanya takalmi goma a kanka kai ɗai,*
*ai da an gano ka sai a ce ga mahaukaci nan,*
*sai dai ka sa guda ɗai haka nan wanda bai da ko ɗai,*
*shi ma i sa guda ɗai, matuƙar in yana da hali,*
*to malam idan ka duba duka dangantakarku daidai.*

A cikin ɗiya ta 6 kuwa, nan ma mawaƙin ya bayyana cewa duk wadatar mai akwai ba zai sanya takalmi guda goma a ƙafarsa shi ɗaya ba, in kuma ya yi hakan kallon da za a yi masa shi ne na mahaukaci. Sannan ya sake kwatanta mara shi da cewa shi ma takalmi guda ɗaya zai sanya a ƙafarsa, matuƙar ya samu dama. Saboda haka, duk mutanen biyun (mawadaci da mabuƙaci) suna da dangantaka guda, domin suna sanye da takalma guda-guda a ƙafafunsu.

**Adabi Yana Fito da Hoton Tunin Wasu Game da Talauci da Wadata**

Adabi yana fito da tunanin wasu game da yadda suke ganin talauci da matalauta kamar yadda suke ganin wadata da kuma mawadata. Wasu mutanen suna ganin matalauta kamar ragwanci ne ya sanya suka zama talakawa, sannan suna ganin mawadata kuwa kamar tsantsar ƙwazon su ne ya sama musu arzikin da suke da shi. Kamar yadda za mu gani a wannan ɗiyar da ke biye:

7. *Kai mai akwai ka gane in ba ka ɗan misali,*
*shi Allah huwallazina bai aiki da duk kuɗinka,*
*bai aiki da arzikinka, sai dai da zuciya fa,*
*haka nan wadda bai da komai,*
*Allah huwallazina bai aiki da babu ɗinsa sai dai da zuciya tai,*
*shin malam idan ka duba ta nan duka dangantakarku daidai.*

A wannan ɗiyar (7) mawaƙin ya ankarar da mai akwai ne game da halin da yake ciki na wadata da cewa ubangiji Allah ba ya dubi da arzikinsa, sai dai yana dubi ne ga abin da zuciyarsa take ƙudurtawa. In ya aikata alheri, za a saka masa da alheri. Haka nan, shi ma talaka Allah ba ya dubi zuwa ga talaucinsa in ya aikata hairan, hairan za a saka masa, duk da cewa ba shi da kuɗi.

**Yadda Adabi ke Ƙokarin Fito da Abin da ke Faruwa, ba Wadda ake Burin Faruwarsa ba**

Adabi yana ƙokarin nuna zahirin faruwar wani abu a haƙiƙaninsa, ba wadda ake burin faruwa ko ra'ayin faruwarsa ba. Wannan ɗiyar ta zo da wannan sigar kamar haka:

8. *Allah huwallazina, kai mai akwai ka gane,*
*in ba ka ɗan misali ran komuwa ga Allah,*
*kai mai akwai ka gane, in baka ɗan misali yadi biyar fari ɗai,*
*a ciki za a nannaɗeka, rami guda akan tona ka tuna ba a tona goma,*
*don wai kana da hali in za a shumfuɗaka,*
*haka nan wanda bai da komai ran komuwa ga Allah,*

*yadi biyar fari ƙal a ciki za a nannaɗe shi, rami guda akan tona,*
*ka tuna ba a tona goma don wai fa bai da komai.*
*To malam idan ka duba ta nan haka dangantakarku daidai.*

A wannan ɗiya ta ƙarshe (8), mawaƙin ya zo da wani salon jan hankalin mawadata domin su fahimci abin da yake ƙoƙarin sanar da su. Inda ya nuna musu cewa su sani fa in suka mutu yadi biyar fari za a nannaɗe su da shi ba za a naɗe su da wani yadi daban ba. Haka nan rami guda ɗaya za a tona domin rufe su a ciki, ba za a tona fiye da rami ɗaya saboda arzikinsu ba. Shi ma kuma talakan ya gane yadi biyar fari za a naɗe shi kuma a ciki rami ɗaya za a tona a sanya shi ciki, ba za a tona rabin rami a sanya shi a ciki saboda talaucinsa ba.

**Sakamakon Bincike**

Wannan shi ne sakamakon da binciken ya gano daga ƙarshe:

1. Sakamakon binciken ya nuna matsayin mai akwai da babu guda ɗaya ne a wurin Allah, saboda duk cikarsu Allah ne ya halicce su. Kuma duk wadda ya mutu nau'in sutura guda (fari) ake yi masa tsakanin mai akwai da babu.
2. Sannan takardar ta gano yadda mai akwai yake kallon maras shi a matsayin cibayayye tsakanin al'umma, saboda mabuƙaci ne shi.
3. Kuma takardar ta gano duk wadatar da mai shi yake da ita, ba zai iya raba kansa zuwa gadaje da ɗakuna daban-daban lokacin da zai yi bacci in dare ya yi ba.
4. Haka nan, lokacin da agogo mai tsadar kuɗi zai bayyana haka nan agogo mai ƙaramin kuɗi ma zai bayyana. Saboda haka duk sunansu agogo.
5. Kuma duk wadatar mai akwai, bai isa ya sanya hula fiye da guda ɗaya a kansa ba saboda wadata, yana yin hakan za a zarge shi da hauka.
6. Sakamakon da Allah zai bai wa mai akwai da mara shi a dalilin aikin da suka yi na alheri ko sharri duk guda ɗaya ne, babu bambanci tsakaninsu domin shi Allah yana dubin zuciyoyin masu aiki ne, ba dukiyoyinsu ba.
7. Daga ƙarshe, hatta rami da suturar da za a rufe mai akwai da babu duk guda (fari) ne, ba a bambancewa, saboda wannan mai akwai ne, wannan kuwa mara shi ne.

**Kammalawa**

Wannan takarda ta yi tsokaci kan ma'anar zahiranci da manufofinsa da kuma ma'anar waƙar baka daga masana mabambanta tare da kawo taƙaitaccen tarihin Alh. Adamu Ɗanmaraya Jos kasancewar an yi aiki da waƙarsa ta *mai akwai da babu*, sannan aka danganta ra'in zahiranci da waƙar tasa. Kuma takardar ta bayyana yadda mawadaci yake kallon mabuƙaci a matsayin malalaci, kasancewarsa mara shi. Daga nan kuma ta yi jan hankali ga mawadaci, da cewa shi kuɗin da yake da shi Allah ne ya ga damar wadata shi da su, ba dabararsa ba. Haka nan shi ma mabuƙaci ba ƙinsa Allah yake yi ba ya bar shi a haka, a'a hakan ya ga damar ganinsa.

**Manazarta**


Ado, A. (2017). *Ra'o'in Bincike Kan Al'adun Hausawa*. Kanki Classical Media Enterprises.
CNHN. (2006). *Kamusun Hausa na Jami'ar Bayero*. Ahmadu Bello University Press Ltd.
Ɗan Maraya - Wikipedia: https://en.wikipedia.org/wiki/Dan_Maraya
Ɗan Maraya Jos Profile and Discography | African Music Library: https://www.facebook.com/groups/2524761247613971/posts/3086956504727773/
Ɗangambo, A. (1984). *Rabe-raben Adabin Hausa da Muhimmancinsa ga Rayuwar Hausawa.* Maɗaba'ar Triumph.
Ɗangambo, A. (2007). *Ɗaurayar Gadon Feɗe Waƙa (Sabon Tsari)*. Amana Publishers Ltd.

Gambo, S. I. (2017). Ra'in Zahiranci a Cikin Waƙar Baka: Tsokaci Kan Waƙar Bakalori Dam na Alhaji Musa Ɗankwairo. Cikin *Jalingo Journal of Linguistics and Literary Studies*. Victorious Publications. Vol. 2, No. 1 (93-105).

Gusau, S. M. (2005). *Makaɗa da Mawaƙan Hausa*. Benchmark Publishers Ltd.

Gusau, S. M. (2008). *Waƙokin baka a ƙasar Hausa: Yanaye-yanayensu da sigoginsu*. Benchmark Publishers Ltd.

Gusau, S. M. (2014). Waƙokin baka Bahaushiya. BUK Professorial Lecture Series No. 14. Jami'ar Bayero.

Gusau, S. M. (2023). *Jagoran Nazarin Waƙar Baka*. Benchmark Publishers Ltd.

Ilorin, J. A. (1994). *Moral Philosophy in Africa Context for Universities and Colleges of Educations*. ABU Press Ltd.

Muhammad, Y. M. (2003). *Adabin Hausa*. Ahmadu Bello University Press Ltd.

Obituary: Ɗan Maraya Jos, iconic Hausa singer and Nigeria's 'best-known' orphan|TheCable: https://www.facebook.com/268230756651167/posts/legend-of-the-day-dan-maraya-josdan-maraya-jos-is-our-legend-of-the-daydan-maray/1116912205116347/

Reymond, A. (1966). *Peace and War: A Theory of International Relations*, Trans. Howard and Anette Baker Fod. Garden City, Doubleday.

Smith, S. (1985). *The New Guide to Modern Literature*. Peter Bedrick Books and New York.

Yakasai, B. S. (BSB). *Modern Comprehensive Hausa Language for Senior Secondary Schools*. Anka Graphics.

Alhaji Adamu Ɗanmaraya Jos

1. *Amma mai akwai da babu duka dangantakanku daidai,*
   *Allah ike faɗan haka ba ni nake faɗa ba,*
   *da ni nake faɗan haka da sai ku ƙaryata ni.*
2. *Kai mai akwai ka gane idan kai gida talatin cikin guda za ka je ka kwana,*
   *a ɗaki guda kakan kwan a kayin gado guda ɗai,*
   *haka nan wanda bai da komai gida guda za i je i kwana,*
   *a ɗaki guda ikan kwan a gefe guda ikan kwan,*
   *a kayin karauno falle, to in gari ya waye ta nan duka dangantakarku daidai.*
3. *In baku ɗan misali kai mai akwai ka gane,*
   *in kana taƙamar akwai ne, ba ka sanya hula goma a kanka kai ɗai,*
   *ai da an ganoka sai a ce wane ya tabu,*
   *sai dai ka sa guda ɗai haka nan wanda bai da komai,*
   *shi ma i sa guda ɗai matuƙar in yana da hali,*
   *to malam idan ka duba ta nan duka dangantakarku daidai.*
4. *In ba ku ɗan misali da agogon jeka talatin, da agogon sulai talatin,*
   *in wannan i ba da loko daidai, wannan i ba da loko daidai,*
   *in za a dai kira su, sai ka ga sunansu duk agogo.*
5. *In ba ku ɗan misali da nonon sulei talatin da nonon kwabo talatin,*
   *in za ka dai sumayi sai ka ga duk dai farinsu daidai.*
6. *Kai mai akwai ka gane, in kana taƙamar akwai ne,*
   *ba ka sanya takalmi goma a kanka kai ɗai,*
   *ai da an gano ka sai a ce ga mahaukaci nan,*
   *sai dai ka sa guda ɗai haka nan wanda bai da ko ɗai,*
   *shi ma i sa guda ɗai, matuƙar in yana da hali,*
   *to malam idan ka duba duka dangantakarku daidai.*
7. *Kai mai akwai ka gane in ba ka ɗan misali,*

*shi Allah huwallazina bai aiki da duk kuɗinka,*
*bai aiki da arzikinka, sai dai da zuciya fa,*
*haka nan wadda bai da komai,*
*Allah huwallazina bai aiki da babu ɗinsa sai dai da zuciya tai,*
*shin malam idan ka duba ta nan duka dangantakarku daidai.*

8. *Allah huwallazina, kai mai akwai ka gane,*
*in ba ka ɗan misali ran komuwa ga Allah,*
*kai mai akwai ka gane, in baka ɗan misali yadi biyar fari ɗai,*
*a ciki za a nannaɗeka, rami guda akan tona ka tuna ba a tona goma,*
*don wai kana da hali in za a shumfuɗaka,*
*haka nan wanda bai da komai ran komuwa ga Allah,*
*yadi biyar fari ƙal a ciki za a nannaɗe shi, rami guda akan tona,*
*ka tuna ba a tona goma don wai fa bai da komai.*
*To malam idan ka duba ta nan haka dangantakarku daidai.*

Recebido em: 23/02/2025

Aceito em: 24/06/2025

**Para citar este texto (ABNT):** AL-MUSAWI, Isa Umar. Ra'in Zahiranci a Cikin Waƙar Baka: Tsokaci a Kan Waƙar *Mai Akwai da Babu* ta Alh. (Dr) Adamu Ɗanmaraya Jos *Njinga & Sepé:* Revista Internacional de Culturas, Línguas Africanas e Brasileiras. São Francisco do Conde (BA), vol.5, nº Especial I, p. 24-32, jan./jun.2025.

**Para citar este texto (APA):** Al-Musawi, Isa Umar. (jan./jun.2025). Ra'in Zahiranci a Cikin Waƙar Baka: Tsokaci a Kan Waƙar *Mai Akwai da Babu* ta Alh. (Dr) Adamu Ɗanmaraya Jos. *Njinga & Sepé: Revista Internacional de Culturas, Línguas Africanas e Brasileiras.* São Francisco do Conde (BA), 5 (Especial I): 24-32.